

DEREK PRINCE
MINISTRIES INTERNATIONAL

Abincin Yini

Kebewa domin Ɗaukaka

Yesu ya ɗauki kunyarmu domin mu sami ɗaukakar Sa



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

"Gama wanda ya rigaya sani, shi kuma ya rigaya ya ƙaddara a kamanta shi da surar Ɗansa, domin shi zama farin haihuwa a cikin 'yan'uwa da yawa. Waɗanda kwa ya ƙaddara, su kuma ya kira; waɗanda ya kira, ya kuma baratadda su, waɗanda ya baratadda su, su kuma ya ɗaukaka. Mi za mu ce da waɗannan al'amura fa? Idan Allah ke wajenmu, wa ke gāba da mu? Wanda ba ya kebe Ɗa nasa ba, amma ya bashe shi domin mu duka—ƙaka za ya rasa ba mu abu duka kuma tare da shi a yalwace?" (Romawa 8:29–32)

Idan muna tarayya da Yesu a cikin mutuwarsa, mun shiga cikin yalwar gadon Sa. Mun zama magada na Allah da kuma magada tare da Yesu Kristi. Amma akwai tsari. Bulus ya tsara matakai biyar, waɗanda duka suna cikin lokacin da ya wuce. Matakan farko guda biyu sun zama madawwama tun kafin lokaci ya fara: Allah ya san mu kuma ya ƙaddara mu. Daga nan, sai Allah ya kira mu ta wurin wa'azin bishara. Lokacin da muka amsa kiran, sai ya baratar da mu. Amma bai tsaya a nan ba; Ya kuma ɗaukaka mu. Ya ɗaga mu domin mu sami ɗaukaka tare da Yesu a sama a matsayin sarakuna da firistoci. Ba a nan gaba ba, amma abin da ya riga ya faru ne.

"Idan fa aka tashe ku tare da Kristi, ku biɗi abubuwan da ke bisa, inda Kristi yake a zaune ga hannun dama na Allah. Ku kwallafa ranku ga abubuwan da suke bisa, ba wajen na ƙasa ba. Gama kuka mutu, ranku kuwa a boye yake tare da Kristi cikin Allah. Sa'ad da Kristi, wanda shi ke shi ranmu, ya bayyana, sa'an nan ku kuma tare da shi za ku bayyana cikin daraja." (Kolosiyawa 3:1–4)


© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Mun riga mun sami ɗaukakar Kristi, amma tana cikin duniyar da ba a gani, ba a gani da ido. Inda Yesu yake, mu ma muna can.

Na gode maka, Yesu, saboda aikin ka a kan gicciye. Ina furta cewa Allah ya riga ya sanni, ya ƙaddara ni, ya kira ni, ya baratad da ni, ya kuma ɗaukaka ni. Yesu ya ɗauki kunya ta domin in sami ɗaukakar Sa. Amin.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-140-HAU
Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026
Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.